DAME AKE ADO

BOOK 2

1 DAME AKE ADO 2 Uban waye yagaya muku wane munafuki ne yasanar daku wannan magana Umma tafadi ahasale batabar sunce komai ba tadora da masifa to duk wanda yagayamuku karya yake yi hassada ce kawai nice nahaifi Ahmad nice uwarsa Afusace take maganar Daya daga cikinsu takuma amshewa haba baiwar Allah kiyi hakuri munriga munji komai zance duniya fa baya buya Idan har danki ne mai yasanya aka cireshi daga lissafin sunan yayan gidan kinada Auwalu da sani da rabi'u yaya akayi shi yafita daban? Mu kinga yansako ne kiyi hakuri sai anjima tadire kudin sadaki akan kayan suka juya suka nufi kofar fita Umma tabisu dasauri tana fadin don Allah kudawo nayi muku cikakken bayani don Allah kudawo Basu saurareta ba suka nifi kofa suna ficewa suna ganin Ahmad suka kalleshi suka wuce kawai Umma data biyosu da sauri arude taci karo da Ahmad tsaye ta yi turus cike da tsanani tashin hankali tana kallonsa Ahmad yana tsaye idonsa yana zubda hawaye cikin muryan kuka yake fadin kirabudasu Umma ki kyalesu gaskiya suka fada munyi laifi dabamu gayamusu gaskiya tun farkoba wannan wace irin masifa ce wane irin cin mutunci ne wannan don cuta sai da muka gama komai harmun raba katin biki zasuzo mana dawannan maganar wane irin Abin kunyane wannan shikam tsananin tausayin Umma yafi komai yawa aransa wane irin so ne wannan baiwar Allah take yimasa ina ma itace tazo a matsayin mahaifiyarsa inama ana komawa baya asauya Uwa daya koma yafita daga cikin mahaukaciya yakoma cikin Ummansa mlm sulaiman dake sallama yashigo da hanzari jin kuka matarsa a rude yake yakalli deeje dake kuka yakalli Ahmad cikin tsananin damuwa yace Ify deeje meke faruwa haka kike kuka subhanallahi Dahannu ta nuna masa tulin kayan lefe dake jibge yakallesu yadawo da kallon kanta yakuma shiga rudu kansa ya kulle yace banfahimta ba deeje ? Cikin kuka tace daga gidnsu Ummi wacce Ahmad zai aura waisun fasa auren ...... Takuma fashewa dakuka yawaro ido waje da wata irin kidima mara fasaltuwa gabadaya jijiyoyin jikinsa sun janye saiji tamkar yadaskare dakyar ya iya karfin halin kakalo wani zancen bangane sunfasa Auren ba wani abu akayimusu tadansausata kukan tana goge hawaye

2 tace ba.ayimusu kome ba mlm saidai munafukai sun shiga ciki lamarin anje angayamusu Ahmad wai shege ne ba shida uba banda wulakacin mai yasanya tunfarko basu ce haka ba saida aka kammala komai malam yayi shiru yama rasa abinda zaice domin iliminsa da tunaninsa suntsaya gabadaya na wucin gadin Lami dake labe tana jinsu tadaka tsalle cike da tsananin murna har da daga hannu sama ta fadi Alhamdulillahi da.anayimin wata fuffuka kullum yaro yana shiga manyan riguna shiga masu gida daman nafadamasa ba da riga ake ado ba da uba ake ado ehe! Takuma zuro kanta tana jiran jin abin da mlm din zaice tasami nadorawa sai jiyo shi yana fadin kunga kuwuce ciki muyi maganar kantabarma suka zauzzauna mlm yadubesu da damuwa yace duk Abinda Allah yakaddara babu makawa sai ya sami bawa daman can Allah baikaddaro ummi matarka bace Ahmad don haka babu yanda za.ayi ka aureta Umma tace Amman mlm baka ganin anbata masa suna kana ganin ko wata diyar yaje aure zata yadda ta aureshi malam ? Ahmad yadafe kai yana kallon umma tausayinta yana kuma karuwa aransa da kyar ya iya bude baki saboda nauyinda yayi masa yace Umma kiyi hakuri kiyi hakuri .......kuka yaci karfinsa malam yadube shi da tausayawa wato Umman yake baiwa hakuri

Umma tace Ahmadu kai ya dace mu baiwa hakuri tunda mun kasa kareka daga wannan suna mummuna mun kasa cire kalmar shege daga jikinka Balaifinku bane ba Umma bakuda laifi kunyi duk wani yunkuri na boye wannan mummunan suna daga gareni Amman Allah yakaddara sai najishi Umma idan wanka ba.aboye cibifa malam yakalleshi da hanzari yace kaga tashi kawuce dakinka zansan yanda za.ayi idan takama aje a sulhunta nema zanyi zannemeka yamike dasauri yana tangadi iska naneman kayardashi saboda juwa akarshen kwanar gidan yaci karo da Lami tana lekensu takalle shi da hanzari saita juya tayi cikin gidanta yabita ka llo cike da mamaki mai tsanani bai san abinda yayima matar nan ba tasanyashi agaba yanufi gidansu Ummi yayi shiru yana tunanin idan yacemata shine zata iyakin fitowa kokuma iyayenta suhanata don haka yace da yaro kace Abdul ne bayan tafiyar yaron da kamar sakan talatin saigasu tare da Ummi fuskarta dauke da tsananin mamaki waye kuma Abdul yake sallama da ita mamakin ta yadada karuwa sanda takula bakowa bane sai Ahmad tsaye ya hade hannuwa akirji gabanta ya yanke yafadi tayi dan dum dum kamar zata koma sai kuma ta dake ta bata rai tace gani yaya akayine ? Tana magana babu ko fara.a

3 tsananin mamaki yacika Ahmad yau Ummi ke masa haka yadaure da kyar yace Ummi babu gaisuwa kenanko? Takara hade rai tana fadin baikamata nagaida mayaudari ba kacuceni matuka Ahmad kasanya nabata lokacina daduk wani tunanina akanka Ashe kai shege ne bakada Asali maganar tadakin kirjin kwarai dagaske idonshi yakuma cikowa da kwalla kamar zaifashe da kuka yakwantar da murya cikin lallashi yana fadin

Ummi yanda muka gina soyayyarmu cikin aminci banyi zantan dan Abu kalilan irin haka zai iya mana itaba...... Takalleshe afusace tana fadin Au kai agurinka wannan yar karamar matsalace kenan amman ka bani mamaki matuka to idan kai ta zama karamar matsala a gurinka kana ganin doka kasance shege bawani abu bane to nikam Allah yasani babbar matsala ce bazanso nahaifi ya ya adinga cewar Ubansu shege ne mara asali ba maganar mungina soyayyarmu kuwa daman can akan tubalin toka da karya muka ginata don laillai dana san kai shege ne da banta lokacina akanka ba na soka Ahmad ashe kai mara asali ne ka boyemini kacuceni wlh kayaudaran .... Saita fashe dakuka 4 DAME AKE ADO ....... Ahmad yaji duk yatsani kansa da rayuwarsa tabbas Ummi tayi gaskiya waye zaiso hada zuri.a da shege mara.asali hawaye dayake ta hadiyewa suka ci gaba da biyo kuncinsa yakasa cewa komai domin bashida sauran abinda fada din Ummi ta kalleshi afusace tace idan abinda ya kawoka kenan nizan koma domin inada abinyi a gida yayi dum yana kallonta da tsananin mamaki da damuwa jiyake kamar ya bita yakamota shikenan Ummi tayimasa nisa haka yajuya yanufi gida baisan yanda akayi yajeba yasandai Allah ne yakaishi Acikin gidama duk wanda akasanar da shi abinda yafaru cikin yan uwansa sai hankalinsa yatashi abinda suke tambaya shin Uban waye yaje yafada duk yanda sukaso ganin Ahmad sulallasheshi abin yatura don ya kargame kansa acikin daki Malam sulaiman kam yajima yayi shiru akan dakali yana tunanin mafita har zuwa lokacin da ya cimma burin tunanin nasa yasanya yaro yakira masa dan uwansa mlm jibril bada jimawa ba ya fito ya zauna kusa da yayansa yace malam gani naji ance kana kira na yakalle shi tsahon lokaci sannan yace kaji abinda yafaru da Ahmad kuwa? Dasauri yace naji wlh dazu na shiga gida Lami take sanar dani Abin kam baiyi dadi ba mlm sulaiman yanisa yace tunda abin nan yafaru nake tunanin mafita har Allah yasanya tunanina yafado kan diyarka Raliya da hanzari yadubeshi yace Raliya kuma mlm yagyada kai yana fadin ita kuwa kamar yanda kasani nima nasani Raliya tazama gagararriya wacce duk wani kokari namu dana yan uwanta yagagara

gyara ta saidai addu.a gashi tayi girman daya dace ace tafidda miji amman anrasa wanda zaifito dagaske yace yana sonta saboda sanya shashanci datayi agabanta hakan nakeganin abune mawuyaci Raliya tasamu miji nutsattse don haka tunani yasanarda ni mezai hana tunda anyi haka amaida ranar auren Ahmad kanta kada acanza komai ayinan da wata gudan amman kai yakagani domin ka fini hakki akanta yayi shiru tsawoh lokaci yana nazari can yadaga kai yakalli yayanasa yace yaya duk abinda kayanke yayi saidai kana gana ganin Ahmadu bashida wata illah da zata iyayiwa rayuwar Raliya illah ?5mlm sulaiman yaduberhe da sauri yace kada kace mini kacikin mutane masu jahilci dakama wani da laifin wasu wlh bagori zanyiwa kaina ba Ahmadu yafi duk yayanda muka haifa nagarta balle Raliya da kai kanka kasan irin abubuwan kunyar da ta daukowa gidan nan auren nasu shi zai zama rufin Asirinsu baki daya jibril ya girgiza kai yana fadin wannan haka yake to Allah yasanya Alkhairi mlm sulaiman yayi murmushi cike dajin dadi yace Amincewarka tafi komai agareni kuma koda hakan batafaruba kayan dakin raliya daman akaina suke tunda dai nine waliyinta dahaka suka rabu ran malam yahaskake yasan yana da damar kara kyautatawa Ahmad da mai dakinsa Adaki yatta Umma tana lazimi da alama addu.a take yiwa danta yasami guri yazauna yana murmurshi yace Allah dai ya.amsa Addu.arki saiki kwanta ki soma bacci Umma tadubeshi damamaki
Fuskarta babu yabo ba fallasa tace malam kenan kana zaton hankulanmu zasu kwanta cikin sauki kuma wannan kankanin lokaci ? Yakuramata ido yana karantar yanayinta yace Amman ai tunda abin nan yafaru Allah muke gayawa ba kyazato zai kawo mana mafita cikin gaggawa tayi saurin yadda da batunsa har daga fuskarta yafimci hakan ta hanyar yin murmushinta tana fadin duk abinda da akace Allah magana takare Amman taimakeni sanar dani wannan Abin dadin yayi dariya yana kokarin tattaro farin cikinsa suyi rabonshi tare yace danki dai yasami matar aure kuma awannan rana za.ayi bada fashi takalleshi datsananin murna da mamaki wacce tagaza boyuwa akan fuskarta tace najima banji labari mai dadin wannan ba dan Allah mlm wacece dan Uwanane ya.amince da baiwa Ahmad auren diyarsa Raliya kinga Asiri yarufu ko ?
7DAME AKE ADO Anacigaba dagudanarda sha anin biki Abba duk yaraba iv ga dangi da abokansa abin mamaki har sanarwa yasa agidan radio itama Umma tadauki dukanin burinta tasanya akan bikinnan hakanne yasanya yadanne zuciyarsa da damuwarshi ake gudanarda komai cikin farinciki duk da bahakanne akasan ranshiba Abinda yabashi mamaki da tsoro ya kuma sanya Raliya tafita daga ranshi baiwuce rashin mutunci datayi mashi cikin soron gidanba malam yayi matukar kokarinsa domin shine yayi duk wasu kayan daki na Raliya akaje akayi jere hatta kayan daya dace ace uwa tayi shine yayi domin lami cewa tayi Auren da akayiwa diyarta na dole ne donhaka ko tsinke bazatayi ba wadanda suka haka suzasuyi komai saidai mutane dayawa sungane borin kunyane domin babu tsiyar dataaje domin Auren diyarta tuncan baya kudinta wurin bin malamai yake karewa balle yanzu datake iyakacin kokarinta na wannan Auren baitabbataba domin acewarta diyarta kalar masu kudice da Asali ba kamar Ahmad fakiri ba Ranar kamu amarya ba yabo ba fallasa tayi kwalliya kamar gaske koda yake yayyanta sunyi mata fada harda mahaifinta da Abban duk da Ahmad duk da Ahmad bahalarta wurin kamun ba yayi farinciki kwarai dagaske da lbr dayaji gurin yara na yadda Amarya ta cashe rawa
------>DAME AKE ADO part 5.
8â£ DAME AKE ADO Karfe biyar daidai motonci daukar Amarya suka iso Raliya tayi wanka duk da batayi wata kwalliyaba amman tayi fes domin wata yayar Lami takama fada tanafadin tunda akadaura ya kamata su watsarda makaman yakinsu surungumi kaddara yaushe za ace akai

amarya haka wannan yasanya tadan kimtsa idonta kemadagas babu alamun kunya itakadai tasan tanadin datayiwa Angon nata narashin mutunci buhu buhu haka akawuce gidan mijinta da ita saiwajen karfe 9 nadare Ahmad yagama kammala shirya kayansa tsaf cikin jakarsa don haka rataya kawai yayi yanufi gurin Ummansa tana zaune arumfa dasauran yan biki basu watseba yadurkusa yanagadin Umma zanwuce inabukatar Adduarku idan nayimuku wani abu kuyafemin don Allah yasunkuyarda kansa jin muryansa tana rawa tamkar zaifashe dakuka idanuwan Ummansa sunciko da kwallah tanajin kamar zata rabu da dantane har Abada Allah yajarabeta da tsananin son Ahmad bata son Abinda zainisantasu saigashi yau Aure zairabasu tayi shiru tsawon lokaci sannan tadaga kai ta kalleshi yana tsugunne kan kafafuwansa Kansa yana kasa Tunda nake dakai banta ganin wani abu na ashsha kona kaico agarekaba nasan Raliya zata iyayin komai domin ta tunziraka ta kuma hasalaka banason jin komai daga gareka sai alkhairi kada kayadda wani abu nabacin rai yafito daga wurinka kayi komai domin kafarantawa" babanka rai kiyayyar mace takaitacciya ce wata rana zata daina ranar daza awayi gari kunfara tara zuria shikenan komai yazama tarihi Allah yayimaka Albarka idanuwansa suka dinga zubdaí ½í¸ inama yanda yake da iyaye nagari sukai masa fada yaji Raliya ma tanada su da Aurensu yazauna lfy daga can saman kansa yaji umma nafadin tashi kaje kada dare yayi Allah yayi maka Albarka yamike sumu sumi yana fadin Amin yawuce shikenan kyau zai bar gidansu zai bar cin abinci Ummansa ya isa kofar gidan nashi da babur dinsa yasauka yatura kofar ga mamakinsa sai yaga kofar abude take donhaka yatura babur dinsa yashiga tundaga tsakar gida yafara jiyo kugin radio ankure wakokin turawan zamani mamaki yacika shi domin dai daga dakin dake kulle wakokin suke fitowa yasan wannan dakin baccin Raliya ne yakada kai yanufi dakinda aka jera kujeru aciki domin yasan dakin da raliya take bazaisamu damar kwana acikiba ko bata rufo kofarba balle dakin abame yake ma har ya kwanta akan kujera yaga dacewar yakoma shagon gidansa kawai da kayansa ya zauna nanne dakinsa da asuba yatashi ya nufi masallaci tayi sallah yadawo yafara lazimi kamar yanda yasaba daman baisanya ran raliya zata tashi tayi sallah ba domin yasan batada wannan tarbiyar sai wajen 10 nasafe take tashi ai kuwa yau dinma hakane saida rana tatake sannan tatashi lokacin tuni yadade da karyawa domin flask yadauka yaje yasiyo musu shayi dayasha yabar mata nata aflask duk da yanacan daki yana hangota ta windo yaga tafito amman abinda yabashi mamaki har karfe goma raliya bata fitoba kuma gidan ba irin na yangun nan bane mai bandaki aciki balle yace tayi Alwala aciki can saiyajiyo sautin radio ansa kidan jiya naturawan zamani yaso yashareta amman sai yatuna yanzu hakkin raliya da tarbiyar ta duk suna kanshi dole yatunatar da ita gaskiya don haka yamike yanufi dakin nata yatura kofa dasallama tadaga kai cike da tsananin mamaki tana dubansa shikam yanayin daya taddata ne yasanyashi tsananin firgita da rudewa domin wata yar figigiyar rigar bacci ce ajikinta dukkan surarta tana waje jikinnan nata yayi jajur tasha man kanti gashi tana kan kurciyarta saiwani sheki da sulbi fatarta keyi 9â£ DAME AKE ADO Wani abu yadinga jin yanaimasa yawo cikin kanshi saboda baitaba baitaba ganin wata mace cikin irin wannan yanayiba yayi masa wani kallon banza sama dakasa tana yatsina fuska tace inazaton kayi batan kaine ko malam yanayin yanda tayimasa maganar yayi gaggawar dawo dashi cikin haiyacinsa yayi kokarin tattaro jarumtakarsa da nutsuwarsa yasanya akan fuskarsa duk da zuciyarsa tayi kokarin bijirema hakan sannan yayi kokarin zakulo abinda yakawoshi inatasau raren ganin kinfito kinyi sallah asuba saikuna naji kin kunna radio ma alamar bakida niyyar gaida ubangijinki Tayi dariya tayi shewa tayi masa irin kallon da akeyiwa

yantasha Au ashe fa Ustazu aka kakaba mini ko? Wai kayi zaton zuwa nayi zama agidanka dan Allah dubeni kadubi fatata aikasan banyi kalar dazan iya zama acikin wannan gidan kirar talakawaba talauci yahaifeni nakuma yadda nazauna natayu acikinsa amman bazan yadda na dauwama har nakare rayuwata acikin saba batun sallah kuwa kada ka matsamini domin ba kabarinmu dayaba bakuma bazo zama bane jira nake kashigo kabani red card dina Ransa yabaci ainun banda kaddara me ye hadinsa da Raliya komai jahila bata iya komaiba sai wauta amman ace itace matarsa takuma zage tana zaginsa haka yayi kamar yakara magana saiyaga rashin dacewar hakan danhaka yajuya da zummar ficewa saiya jiyota daga bayansa tana fadin malam fitafa bata kama kaba gwara kasallameni tunban yagama rigar mutuncinkaba baikulataba yafice domin tunaninta irin na dabbobine idan yaci gaba dajinta komai na iya faruwa kawai sai yafice daga gidan yaukam abin yafi najiya domin tundaga kofar gida akejin sautin kida yashiga da sallama badon yasan zatajiba sai domin mutanen boye abin mamaki saiya hango takalmi barkatai na mata dakuma hayaniyarsu anata shewa ga tukwane da kwanuka Nan anyi girki anbata gidan yayi faca faca harda garar abban

DAME AKE ADO part 7.
duniya tayi mata yanda takeso kenan tsawon sati guda kenan anazaman yan marina agidan babu wani da Raliya dakeyi na zaman Aure hatta shara shiyakeyinta wanke wanke kawai take yi shima dan ita take bata kwanikan da kawayenta dake wuni kullum agidan dayafita aiki sukuma zasu dira basu barin gidan sai dare zuwan Lami nafarko kuma nakarshe shiyakara dagula komai suna daki ita da diyarta sunata kulle kullensu ya iso gidan agajiye yake tubus domin yau bai tsaya hutawa ba kamar yanda yasaba yana rashi daga aiki yayo gida kawai kai tsaye yashigo da babur dinsa gidan Dai dai lokacin da yaji Lami tafito daga dakin Raliya nabiye da ita furucinta nakarshe ne ya doki dodon kunnensa1️⃣2️⃣DAME AKE ADO 2 Yayi tsai yana jiyo ta tana ta habaici da zage zage dukkan kalamanta bakomai bane illa tunin kalaman da mahaifiyarta kegaya masa sanda yana yaro har ya girma bashida abinyi bayan neman tsari daga shaidan dan kada yatunzurashi ya aikata abinda zaisanyashi dana sani agaba yana jin kiran sallah magriba yayi sauri yafice dan bada farali acan masallaci ya zauna yana lazimi har akayi sallar isha I yayi sannan yanufi wani gidan Abinci namasu karamin karfi yaci yakoshi ya jima agurin yana tunane tunane domin yarage dare fatanshi sanda zai isa gidan Raliya matar jaraba tayi bacci don haka sai wajen karfe shadaya yanufi gidansa ya tura kofar a hankali ya shiga yamaida kofar yarufe cikin gida yawuce yadauro Alwala domin dai yau daren jumua ne waton ranar Alhamis daren da Allah kanyi saurin amsar Addua bayinsa don haka yayi Alkawarin kaima Allah kukansa shima yau yazabamasa Abinda yafi Alkhairi yana sallah yajiyo bugun kofar raliya kamar zata balle masa kofar abinda yabashi mamaki biyu ne na farko kofar abude take amman taketa dukanta nabiyu kuma me yakawota dakinsa saidai yakula bazata barshi yayi sallah nan idan har baikulataba dan da karfi take bugun kofar tayi kokarin yin sallam yanufo kofar yadubeta sanda take kallon sa tadaina dukan kofar cikin tsananin mamaki yace Ify takalleshi araine tayi wani tsaki zuwa nayi Amsar sallamata domin nagaji dazama wannan akurkin naka nakula bakada zuciya domin kare yacinye dazai iya dayanzu zaiyiwa Raliya saki dubu sai dai bazai iya baiwa iyayensa kunya ba amman yau yakamata ya nunawa raliya shima fa baya kaunarta ko sau daya cikin kallon isgilanci yace waikina zaton ina zaune dakene dan kyawon fuskarki ko kyawon jikinki kiwata dabia maikyau dana gani agareki kiyi sani kamar

yanda kika tsaneni kika kuma tsani aure na kodon inasonki a a kodaya nima haka nakeji harnawa ya linka naki tayi shewa da dariya tana kallonsa cikin tsakiyar idonsa da tsananin raini da wulakanci Ahayye wannan shi akecewa shege yi da maizina kaiko rayiwarka kayace nikam zan iya duk abinda naga dama nadawo natuba nakuma Auru sabanin kai da anriga anrubuto kai shege ne babu kankara shut up stupid yadakamata wata irin gigitacciyar tsawa data sanyaya firgita yaci gaba damagana cikin bacin rai koda nakasance shege wlh nafiki Albarka damutunci a idanuwan kowa dabba shashasha kiyita gorin naki dafadar abinda kikaga dama domin halinki irin na wawaye ne jahilai amman kisani idan har ga hannuna saki yake bazan taba sakinki ba sokuwa kawai yajuya dazummar komawa cikin shagon saidai riko wuyan rigarsa datayi tabaya ne yasanya yakasa cigaba datafiyar tarikeshi katamau tana fadin wlh ba indazaka saika sakeni meye kawai banda naci banason aurenka dolene wlh yawon karuwanci yafimin wannan kalgaggen auren naka zuciyarsa yadinga zillo datafasa afusace ya banbare hannuta cikin zafinrai ya hanbareta tayi taga taga tafadi warwas akasa tayi karo dabango tafasa wata kara domin hannunta yabugu da alama tayi targadema tafashe dakukan azaba ya kalleta dajan ido yana fadin sokuwa kinyadda duka guda zai iya maganinki kisani bawannan rayuwa ce agabanaba tadabbobi inada hankali da tunani idan har kinason rabuwa dani kije can kisami can wadanda suka daura kisanar dasu yamaida kofar yarufe raliya kam dakyar
tatshi daga faduwar datayi tanakuka sakale da hannuta saidai bakinta bai mutuba taci gaba datijara ta Allah ya isa shege tsinanne dan mahaukaciyar kan bola daba asan aslinsaba duk abinda yazo bakinta fadi takeyi afatanta nata tunzirashi yafadi kalmar saki agareta kamar yanda Lami tabata umurni tagayamasa kalaman dazasu tunzirashi amman baice uffanba saidai hawaye

DAME AKE ADO part 8.

baice uffanba saidai hawayeí ½í¸í ½í¸ dayake zubdawa yana tasbihi ga Allah afili dazuci harzuwa lokcin datagaji datijarar takama hanya tawuce dakinta tana kukan bakinciki kukan nata kashi biyu ne nafarko narashin cikar burinta nasakinta dayakiyi nabiyu kuma nabugewar datayi hartayi targade dayadaina jinmuryarta saiyamike yaci gaba da sallarsa yana kuka yana sanarda Allah halin dayake ciki

..........DAME AKE ADO 2 .................Saiwajen karfe 3 dawani abu nadare yaji gwiwoinsa sunyi sanyi idanuwansa sunyi nauyi babu abinda yake bukata illah yakwanta yahuta don haka yayi addua yakwanta bisa tabarmarsa cikin kankani lokaci kuwa bacci yadauke shi saboda rashin bacci daibaiyi da wuriba yasashi yamakara baitashi da asuba yayi sallah ba saida hasken rana yashigo dakin ta wundo ya haskemasa ido sannan yafarka afirgice ya duba agogon dake jikin wayarsa saiyaga yanuna karfe 7 nasafe yamike dasauri yana istigfari yanufi kofa yabude kaitsaye cikin gidan yanufa don daura Alwala abinda yabashi mamaki yau baiwuce rashin jiyo sautin kidan raliya ba wanda kullaum dashi take farkawa kamar shedaniya yashiga yakama ruwa yadawo yatsuguna gundi rariya yana daura Alwala yana satar kallon dakin nata yana adduar Allah yasanya harya gama Raliya batafitoba domin bayason ko kallon fuskarta cikin ikon Allah kuwa har yakammala din bata fitoba yanufi shagonsa yayi tusur cike datsananin tsoro domin ganin kofar gidan abude abinda yabashi tsoro kuwa tunda suke agidan raliya bata taba bude kofar gidaba yawaiga cikin gida saiyaga babu takalman Raliya akofar dakinta dasauri yadaga labule gamamakinsa saiyaga duk anwatsar da kaya acikin sif dakin yayi kaca kaca da alamar andibi wasu kayan gabansa ya kuma faduwa badai gudowa raliya tayiba dagacan kan

gado yahango wata takarda ayashe ya isa dasauri yadauka yabude cikin wani cukurkudadden Rubutu yaga sakon nata yafara karantawa BAKA BUKATAR SALLAMA DOMIN BATA DACE DA SHEGE IRINKABA DUK WASU HANYOYI DA NASAN ZAN IYABI DON GANIN KASAUWAKEMIN WANNAN KALGAGGEN AUREN NAKA NABI AMMAN KAKI SAUWAKEMIN DON HAKA NABI HANYAR DATAFI DACEWA WATON NAGUDU NABARKA DA AURENKA IDAN KAGA DAMA YANZU KA IYA AIKAMA IYAYENA DATAKARDAR SAKINA DOMIN SANDA ZAKACI KARO DAWANNAN TAKARDA TUNI NAYIMAKA NISA KAIDA RAYUWARKA SAIKUMA ACIGABA DAZAMAN GAURANTAKA DONNASAN HARKA KOMA GA ALLAH BABU MACEN DAZATA YARDA TA AURI SHEGE BA .SAIWATA RANA RALIYA yaruntse idanuwansa sanda yakai karshen takardar sako mafi muni dazafi da idanuwansa suka tabacin karo dashi yajima tsaye yana tunanin meyadace yayi farincikin rabuwa da Raliya ko kuma bakin cikin gudunshi datayi
1â£5â£ DAME AKE ADO2 Mlm jibrilu ne yafara tambayar yaya akayi yaya Allah dai yasanya lfy domin naganku cikin damuwa malam sulaiman yamika masa takarda yana fadin karanra kagani malam jibril yakalli takarda batare da ya amsaba yace yaya aikasan ban iya karatun boko sosai ba danhaka bana gane kowane rubutu balle wannan danake ganinsa kamar zane tsutsotsi mlm sulaiman ya gyara tsayuwa yanuna masa takardar yace kaga wannan takardace da raliya ta rubuta kafin tatafi yawon karuwanci mlm jibrilu yadafe girji dadamuwa yaya wane irin yawon karuwanci kuma A iya sanina Raliya tana gidan mijinta naji dadi dakace a iya saninka alama bakasan gaibuba kenan to kabuda kunnuwanka dakyau kaji Raliya tabar gidan amadu yau da asuba bayan duk tayi wani cinmutunci dazagi baikulataba tabar wasika takuma ce dazaman auren Ahmadu gara taje tayi karuwanci yafiyemata kaga abunda nake nusar dakai tun abaya ko? Mlm jibril yayishiru cike da tsananin damuwa yamarasa mezaice dan idanuwansa sunkada suyi jajir gwanin bantausayi itakuwa Lami babu wata damuwa ko kyas atare da ita saiwani fici fici take da idanu irin namarasa gaskiya tana kara tsare gida mlm jibril yace yanzu to yaza ayi kenan kobin sahunta za ayine? Abita ina Raliya bayarinya bace tunda har taiya hada kayanta tagudu takuma furta kalmar tafiya karuwanci abin yakai intaha saidai Abinda tace Ayau zankaryatashi da tace sai dai Ahmadu yamutu babu Aure to tayi karya itace zata mutu babu Aure ba Ahmadu yaron kirki ba taje duniya fadine da ita wanda baizobama jiransa take yakada kai yashige dakinsa yana huci Umma kam saicika take tana batsewa tamkar tashako lami domin tariga tagane dasanya hannun lami takuta tace idan anguji dan wata illah abanza domin shi baida laifin kimai wanda kuma yake aikata irin laifin kumafa ? Karuwanci sana ace babba mai lasisi saidai tanada darussanta muna zuba ido muga karshen butulci darashin tarbiya lami takulu da kalaman umma tayamutsa fuska tana fadin oho kome za afada taba tarago tunda aibamu mukace raliya tatafiba duk kuma inda take Allah ne zaikareta Allah bazaikare Raliyaba lami yarinyar data tafi da hakkin mijinta da Aurenta kike zaton zatasamu kariyar Allah wlh ta barranta daga rahamar Allah bakuma zanyafemata wannan tozarci da cinmutunci dajamini ba Ahmadu dayake namiji yayi hakuri amman ita takasa taje duniyace mlm jibril yakarasa maganar tamkar zairushe dakuka domin yana ganin iyakacin tozarci raliya tayimasa Lami takuma cika afili tace Allah dai shike raba rahama ba mutumba mlm jibril yabita da kallo kamar yashakota amman saiya dake yakyaleta ya gyada kanshi yana kallon kofar dakin yayansa yace malam kafito mukarasa maganar nan kayi hakuri Ahmad dai yana durkushe yana kallonsu.
DAME AKE ADO part 9.

16 DAME AKE ADO 2 Daga masallaci makarantar su Asma u yanufa yadaukota daga can bakin kofa yaji wata sinio tana kwala mata kira Asma'u sulaiman tana ina tamike dasauri jikinta yana rawa tayi zaton wani laifi tayi kokuma dealing dinne yamotsa na sinio hajara domin shegiyar kazamace kayanta har tsami suke dahaka takwace kanta da maryam kemata kalbar da maryam keyimata tanufi wurin sinio hajara tana fadin tanafadin senio hajara gani senio hajara takalleta sama da kasa da alama yarinya uwarki ko ubanki sun mutu domin sir Abdul yace kije kitafi da dukkanin kayanki domin gidanku zaki wuce ma'u tadafe kai cike da fargaba sai tafashe da kuka tana fadin wayyo nashiga ukku Allah yasanya ba umma ko abba bane suka mutu ba wayyo Allah ni ma'u nazama marainiya ihu takeyi iyakacin karfinta gabadaya hostel akayi shuru anakallonta kawayenta tuni sun iso inda take dasauri suna tambayar abinda yafaru senio hajara takama masifa ke sakarya nibance miki wani naki yarasuba cewa nayi kawai inajin kihado kayanki muwuce kusai kutayata debo kayan nata ta kalli sauran kawayen nata dasauri ma'u tanufi gurin kayanta taci gaba da hadawa tana kuka sosai kawayenta suna bata hakuri da rarrashunta sanda suka isa wurin sir Abdul yakalleta damamaki yana fadin ma'u meyasanyaki kuka? Cikin sheshshekar kuka tace senio hajarace tace wai babana ko ummana sunmutu yabata rai matuka yace inji ubanwa? Hajara tanada matsala kawai nace kihado kayanki babanki zaitafi dake shike nan zatace haka barta kawai karya takeyi hankalin ma'u yadan kwanta saidai tana cike da tsananin mamakin abinda zaisanya babanta yazo daukarta bayan anfara jarabawa bukin yayanta kuma ankammala tuni domin alissafinta yau sati biyu kenan da bikin yayanta kokuma dagawa akayine dawanna tunanin tayi sallama dakawayenta sir Abdul yadaukar mata wasu kayan su maryam da jamila suna bata sakon abinda zatasawomusu idan zatadawo tana cewa to batasan wannan ce rana takarashe dazata kara komawa wannan makaranta ba dasunan karatu ba yaune dazata rabu dakawayenta rabuwa tahar abada kuwa ta isa ta tadda abbanta zaune a ofis din principal suna wasu magunguna dabata fahimci komaiba hankalinta yadan kwanta saboda ganin abbanta bakuma cikin wata da muwaba ta durkusa tagaisheda abbanta tagaida principal Abban nata yamike yana fadin to hajiya nagode Allah yataimaka yakuma kara daukaka principal tamike tana fadin Ameen amman munyi missing daliba maikwazo da hazaka Ubangiji yatsareta aduk inda take malam yace Amin dasauri principal tadaga kan ma'u tana fadin Allah kaddara saduwarmu kidage bisa kyawawan halin danasanki kinjiko? Itadai ma'u to kawai take cewa batasan me ake nufiba abbanta yadaukar mata wasu daga cikin kayanta tadauki sauran suka nufi titi sanda suka isa gida anata kiraye kirayen sallah magriba Umma tana kicin tana kokarin hura wuta da alama tayi daren tuwo ne tajiyo sallamarsu ta mike da mamaki tanafadin malam kamar muryan ma'u nakeji mamaki yakoma karuwa ma'u cedai biye da Abbanta yakalli Asma u yace bakama bace deeje itace yanzu na daukota daga makarantarsu mamaki yakoma cikata tace malam amman banji Ibr anyi hutuba naji kamar jarabawa suke ma Ify yanufi kofar bandaki ya dauki wata buta da aka ajiye daruwa yana magana Ify kalau kidai kiramin dukkan yaran gidannan awaya kice inason ganinsu idan nadawo daga masallaci zakiji karin bayani yashige cikin bandaki don yakama ruwa Umma tamaida kallonta ga ma'u kamar zata koma tambayarta sai kuma tafasa tace shiga dakayan cikin daki kizo kidaura Alwala ma'u tayi abinda mahaifiyar tata ta umurceta bayan tacire uniform din dake jikinta tasake kaya tafito ta daura Alwala itakuma Umma kokarin fara kiran wayoyin yaran gidan ta isar da sakon da mahaifinsu tasanardasu sannan tadaura Alwala tashiga sallah

17 DAME AKE ADO 2 Har suka kammala taruwa malam din baishigo ba domin saida ya tsaya

yasiyo goro da alawa yataho dasu suna tsakar gida bisa babbar tabarma anata tattaunawa akan maganar gudun Raliya Rabiu yace wlh dani tahadu dashi datuni Ibr yasha bamban shegiya kodaddiyar banza kawai taje indai duniya ce wanda baizobama jiransa take shidai Ahmad jinsu yake yana jin tamkar Anrabashi da wata babbar masifa ne arayuwarsa domin kallon raliya bayason yakoma yi yasan Allah ne ya.amshi adduar sa yayi gaggawar rabashi da ita saidai kamar yanda tace din yasan shida aure har abada domin bazai iya kara tunkarar wata mace da sunan yana sonta ba balle haryajawa kansa wulakanci ba zaici gaba dazama ahaka idan yaji zai takura sai yayi azumi Sallamar malam dince ta katse musu hirar su Ahmad yamike da sauri ya amso kayan da malam din yashigo dasu yana fadin sannu abba yakarasa yazauna akan tabarma da yaran ke kai daya bayan daya suka dinga gaisheshi ya .amsa sannan ya kalli Umma yace ina ma'un take kuma? Umma takalli kofa tana cikin daki kasan indai yayanta suna hira bata fitowa cikinsu tazauna wata kilama tayi bacci kotayi bacci atasota yakalli kofar dakin ma'u Asma'u kina inane tafito dasauri tana goge idonta inaciki Abba kadawo sannu dazuwa ya.amsa yauwa samu wuri zauna sannan yaturawa Umma buhun Alewa da goro dake gabansa yana fadin bude kigani deeje Umma taja buhun tafara budawa tadaga kai takalle shi da mamaki goro da alewane kowakilcin Aure zakayi kodaya goron daurin Asma'u da Ahmad ne an daura tundazu a masallacin jumu'a na gidan maimartaba mamaki yakama kowa har akarasa mai iya karfin halin.

DAME AKE ADO part 10.

Umma ce tafara karfin halin yin magana tace malam kaji abinda kace kuwa ? Malam ya gyara zama kwarai da gaske saidai idan kece bakiji ba nasake maimaitamiki goron auren diyata Asma'u da Ahmad ne wanda aka daura dazu a masallacin gidan sarki Ahmad yaji wani abu dim akirjinsa tamkar ancaka masa mashi gabadaya kuzari da tunaninsa ya kwace yama rasa meyada ce yayi Auwalu yayi kokarin yin magana cikin yaran Allah yasanya Alkhari yakuma zaman Ify da zuri'a dayyaba gabadaya suka amsa da Ameen sani yace baba yabatun karatunta kuma wannan yana hannun mijinta dukkan hukunci da yazartar shine daidai daman karatun badole bane ba

18 DAME AKE ADO 2 Umma ta girgiza kai tace hakane to yanzu yaya za ayi kenan malam Gyalenta zata dauka tayafa suwuce gidan mijinta wannan goron kuma da alawar kirabashi gidan makota domin suma sushaida Ahmad yakalli abbansa Afirgice daidai lokacin da Asmau takalleshi itama saitake ganin abin kamar amafarki anya kuwa dagaskene haka daman ake aure Umma takwantar da kai tace malam da anbari har ashirya ahankali sai akaita yadaga mata hannu babu wani shiri dazaayi kidauko mata hijab dinta suwuce da mijinta duk wanda kika aikawa da goron kice har tatare gidan mijinta fakat akayi shiru babu mai abincewa malam yadubi Ahmad wanda yakasa motsi tamkar anzare masa dukkan lakkar jikinsa yace tashi Ahmad kama matarka kuwuce gidanku Ahmad yayi firgigit yamike har alokacin yana tsammanin zolayace amman yasan Abbansu bayamasa irin wannan wasar Umma tamike tashiga cikin daki tadauko hijab tamikawa Asma'u tana fadin Allah yayimaki Albarka yabaku zuria dayyiba yasa Anyi kenan sauran suka amsa da Amin ma'u ta amshi gyalenta tasanya takasa yin komai don tsabar fargaba kamata kuwuce mana malam yakara basu umurni Ahmad saiyake ganin da kunya yakama hannun ma'u musaman da malam ya ambaci matarsa ce wai ayau don haka yawuce dasauri yanufi soro agobe yake kokarin yatattara kayansa yadawo rayuwa da ummansa

ashe bashida rabon sake zama tare da ita wato yabarta kenan har abada Umma takama hannun ma'u domin takula duk tarude tarikice gabadaya abinda kedamun umma dayane yanda bata taba koyarda ma'u komai na rayuwar gidan mijiba atsammaninta saitakara girma takara wayo da hankali ashe bazatakai wannan lokacin ba ayimata aure ba bata tsammanin kofar shinkafa ma'u ta iya dafawa wannan kadai shine abinda zaidameta har abada har saida takaita bakin zaure sannan tatsaya tana fadin maza wuce kutafi Allah yayi muku Albarka

Malam dasauran yaran suka taso suka rakosu hargaban babur din sannan yakarkatamata takama ta hau yatuka suka tafi suna daga musu hannu malam yadubi sauran yace to masu iyali suwuce gidansu kukuma marasa iyali kushiga kutaya mahaifiyarku kullin kayan daurin aure nizan wuce gidan malam habu nasanar dashi dahaka yawuce suma yaran kowa yakama gabanshi sai samari dakanana ne suka shiga cikin gida suka fara din Salisu yace Umma waidaman kunshirya hakanne da Abba bakusanar damuba Umma tagallamasa harara tace bansaniba tambai sarkin tambaya sainaji matsa zanbaka Amsa yanda ta amsa maganar afusace yadan bashi tsoro yace Allah yahuci yahuci zuciyarki Umma kiyi hkr hakan datayiwa salisu yasa kowa yakunshe tashi acikinsa saiwani lokaci Ahanya suna tafe bisa babur kowa da abinda yake sakawa cikin ransa itakam ma'u har lokacin bata yadda ba mafarki takeba domin ko alittafin hikaya bata tabajin irin wannan Ibr maiban mamaki ba shi kam Ahmad jinjina kyautayin da karamcin bayin Allah nan ne aransa dama zai iya sakamusu da karamcin dasuke yimasa waye zai iya aikata irin wannan abin dasuka aikata awannan zamani daya lalace darayuwa irinta jari hujja tabbas sai antona harsuka isa kofar gidan kowa yana sakawa da kwancewa yatsaida babur din yasauka yarike yana fadin sakko19 DAME AKE ADO 2 Yakalleta da kulawa saiyaji duk kunya dafargaba sun kamashi wai ma'unsa kanwarsa yau itace tazama matarshi Allah sarkin iko dabuwaya yadaure yacemata muje mana Tashige yanabinta abaya har suka isa kofar yasanya makulli yabude suka shiga tatsaya atsakar gidan tana karemasa kallo bata kawo komai arantaba sai daman anshirya komai itace kawai ba asanarwa ba tunda gashi har gidan antanada ansanya komai yakalleta amman baibari sunhada idoba yace kije dakin can kiyi sallah ki kwanta dasauri tace to tanufi dakin kamar wacce ke kan kaya daman yabita dakallo har tashige sannan yanufi dan dakinsa shago yasamu wuri yazauna yadafe kumatu Raliya ta tafi Asma'u tashigo shin ita wanne irin zama zasuyi kenan ko amafarki baitaba hango wannan ranana balle idan yafarka yayimata wani nazari hakan yasanya yakasa tabuka tunanin komai sai gyada kai kamar dan kadangariya tana shiga daki tazauna gefen gado tana karewa dakin kallo daga gani natane sabuwar amarya amman yaya akayi ba asanarda ita komaiba duk wani shirin da akeyi meyasanya sanda yaje baisanarda ita cewar za ahada auren su ba sai yabata Ibr Aurensa da Raliya amman da alama shima baida masaniya akan komai tuno raliya datayi yasanya zuciyarta yin kunci waton daman ita kishiyar raliya ce a iyakacin tunaninta bata taba tunano zasa hada miji da Raliya ba meyasanya su Abbanta sukayimata haka tadafe kirjinta yana bugu kamar zaibullo yayo waje idanuwanta suka ciko da kakwalla jikinta yadauki rawa saitakejin kamar ana likamata kiyayyar raliya aranta kishi maigirma yarufeta saita fashe dakuka meya sanya rayuwarta tazomata da wannan akasin itama matar yayanta Ahmad ce tadade tana kukanta kamin tayunkura tafito tsakar gida tadauro alwala takoma daki domin yin sallah ta idar da sallah tana kallon dakin tana lazimi tana sakawa da kwancewa harzuwa sanda tagaji tamike da hijab din jikinta dakomai tahaye gado takwanta saidai me haushin karnuka datake jiyowa akan titi dakukan gyare sun sunhadu sunbirkitama ta tunani sun assasamata tsananin tsoro

bata taba kwana ita kadai adakiba idan tana gida tana makale bayan ummanta har bacci yadauketa sai cikin dare umma ke zamewa tagudu dakin maigidanta da anyi kiran sallar farko tadawo takwanta amakaranta kuwa dakinsu su goma shatara ne don haka bata taba kwana itadaya ba ta mike dasauri tana waigen dakin tome yakamata tayine shin yayanta yakamata takira kokuma rufe kofa zatayi harta kama kofa zata tura saitaji kamar anmata kuwwa cikin kunnen ta danhaka tafito daga cikin dakin dasauri danma dahasken wutar nefa tajima tsaye atsakar gidan tana sakawa da kwancewa tarasa madafa saitaga kamar gidan yana yimata gizo dan haka tayi soro dasauri yayi sa a kofar dakin nasa abude take dan haka tasamu guri ta tsuguna tanannade jikinta cikin hijab tamkar maijin sanyi ahaka har bacci yafara daukara

20 DAME AKE ADO 2 Ahmad yanaciki baisan abinda kefaruwa asoronba tunda yazauna yakasa motsawa yarasa abinda yadace yayai tsawon lokaci yana awannan halin hardare yafara ja saiyaga dacewar yatashi yadaura Alwala yayi sallar isha'i sannan yanemi yardar Allah da amincinsa bisa wannan auren dayazomasa bagatatan yamike yanufi kofar dakinsa yayi baya tsorace yana ambatan sunan Allah domin karo dayaci da ma'u wacce keta shirgan baccinta haikan babu wata fargaba saida yanutsu sannan yasan itace mamaki yakoma kamashi yamatsa kusa da ita yanakallonta meyakawota nan meyasanyata bacci ahaka cikin daga murya yafara ambaton sunanta domin yaga alamar batasan dashi agurinba tafarka afirgice cike da tsananin tsoro dafirgita tana waige waige yadurkusa agabanta nine nana kwantar da hankalinki meyakawo ki nan kina bacciya yafada cikin rarrashi domin yakula duk akidime take tayi narai narai da idonta domin tana tsoron kar yadaketa Allah yaya tsoron dakin nakeji sai naji kamar anamotsi abayan kyauren yayi murmushi yace nana haryazu ke sokuwace ko? Tomeyasanya baki sanar da niba tasunkuyarda kai tanasosa keyarta cike da tsananin kunya yakula tunda suka iso gidan ma 'u kejin kunyar hada ido dashi shima nauyinta yakeji kwarai dagaske jinbata niyar cewa komai yasanya yamike yakama hannunta yanafadin taso muje ki kwanta kada kikara kwanciya anan bamusu tabishi amman hankalinta amman hankalinta yatashi saboda rikemata hannu dayayi saiya sanya tsikar jikinta tashi ahaka harsuka isa dakin yazaunarda ita gefen gado yanafadin to kwanta bari nakwanta akasan yadauko filo daya daga kan gado yajefar kan tayal yakwanta yajuyamata baya Umma tana kwance datsananin damuwa idonta nazubda hawaye batasan sheshshekar kukanta yabaiyanaba malam yamike zaune yakunna fitilar dakin yakalleta duk da tajuya masa baya yasan ba bacci takeyiba cikin raunanniyar murya yakira sunanta khadija kitashi nasan ba bacci kikeba tashi kisanarda ni dalilin kukanki tsoro dafargaba suka kamata ashe kukanta yabayyana har malam yajiyota tashiga ukku meyadace tayi yanzu nace kitashi muyi magana khadijah tsawarshi tasanyata mikewa dasauri jikinta yana rawa domin takula ran malam yabaci yatsareta da idonshi wanda yakada tayi jajir kisanardani abinda keranki khadija kigayamini komai da bakinki cikin rawar murya tace wlh malam bakomai araina karya kikeyi akwai abinda keranki deeje mutum bayayin kuka kawai saida damuwa nalura dake tunda nasanar dake auren ma'u da Ahmad yanayinki yasauya furkarki tanuna bakiji dadin hakaba shinkina kyamar Ahmad dan bayada ubane kece kike nuna jin haushin abinda wasu kemasa kamin wannan lokaci deeje baibarta tabada amsaba taci gaba dafadansa idan harkikayi haka kinbani kunya kinkuma ci Amanar ahmad Ahmad zaitabbatar da lallai bashida uwa bashida galihu kowa yana kyamarsa yakarasa maganar da kunci dazafin zuciya tadaga kai tanafadin kodaya malam wlh abinda kake zato nahaka bane bantaba kin Ahmad ba

21 DAME AKE ADO 2 Bantaba danasanin kasancewarsa tare daniba bantaba danasanin

zamanshi danaba haka banajin komai game da aurensa da ma'u kukan dakaga inayi banakin aurensu bane illah tausayinsu gabadaya Asma'u yarinyace karama bata iya komaiba saiwauta da tsiwa bankoyamata komaiba na rayuwar aureba nayi sakaci bantaba bata Ibr meye aureba shikuma Ahmad yarone dabaisan komai gameda rayuwar aureba shin yaya zai kalli ma'u da halayenta inatsananin jin tausayin ma u dakewarta wlh wannan shine kadai abinda ke damuna amma har abada bazantaba dana sanin hada auren nan da akayiba nayi mamakinma da wannan zargin yazo ranka malam takarasa maganar datsananin damuwa yayi ajiyar zuciyar cike dagarinciki acikin ransa yana godiya ga Allah dayasanya ba abinda yake zargibane aran deejen ba yakalleta yayi murmushi Amman shirmenki yayi yawa waton har abada mace bata girma danwannan abinne kawai yasanyaki damuwa kodayake nasani harda soyayyar ma u dakukan rabuwa da itako yakarasa maganar da zolaya tasunkuyar dakai tana murmushi kasa kasa malam yaci gaba dajawabi kikwantar da hankalinki daga Ahmad har ma'u duk rainonkine watakima ahmad yafiki sanin halayen ma 'u dan haka babu wani abu dazaibiyo baya insha Allah sai Alkhairi nayi imani zaikoyarda ita komai tunda kinkoyamasa kokin manta da dannaki ya iya girki kala kala ne? Yakarasa yana dariya abinda yasanyata darawa itama ya dinga zolayarta haryasamu ta sakko Suka fahimci juna sannan suka kwanta baccinsu sunawa yayansu addua tunda asuba yatasheta tayi sallah shikuma yawuce massalaci bayan yadawo yazarto dakin yazauna yacigaba da lazimi itakam baccinta takara komawa aranta tanaganin babu abinda yafi gadonta dadi kamar wacce akatasa karfe bakwai tafarka ta tadda yayan nata har lokacin yana lazimi tamike tsam tanufi kofa ya bita da kallo kamar zaiyi magana saikuma yafasa don yayi zaton bandaki zatashiga itakam kicin tawuce tayi zaune tanasakawa da warwarewa akan abinda yakamata tayi domin sanda yatafi masallaci umma takira wayarshi tadauka umma tace waye tace nice tace yauwa daman kedin nakeson kidauka domin nasan yanzu Ahmad yana masallaci kinaji idan gari yawaye kishiga kicin ki girkamuku abinda zaku karya sannan kishare gidan kigoge ko ina nasan kin iya shara daguga dan kinayi amakaranta ko dasauri tace eh inayi tace to kitabbatar kinyi kinjiko?
22 DAME AKE ADO 2 Takoma amsawa da to shine yanzu tana tsaka da bacci maganar Umma tatasheta tadauko doya tafara ferewa bayan takammala tayankata gutsi gutsi kamar zatayi faten doya sannan tadauki kwai ukku tafasa akan doya ta kunna risho tadora mai kozafi baiyiba takama kwan da doyar ta zuba tana jiran su soyu daga can acikin daki yafara jiyo kauri dasauri yamike domin zuciyarsa tabashi ma'u ce yanufi kicin din dasuri saiyaga doya da kwai da mai sunata zabalbala yarike baki damamaki yana fadin Nana mezakiyi? Mekike dafawa? Tayi firgigit ganin kallon dayake mata tace doya da kwai zanyi sai akacemiki kuma haka akeyi waye yasanyaki girki kuma baki iyaba cikin zafin rai yake maganar tayi kwal kwal da ido tana jada baya domin tana gudun kada yadoketa tace Umma ce tace nayi abincin Kari kuma............kuma..........yadoka mata tsawa get out mekika iya bayan shirme yadauko kaskon suyar daga kan wuta yayi waje dashi sukaci karo abakin kofa tana tsaye tana gunguni yayi baya dasauri dan sauran kiris yakifamata yakoma kuluwa yace Amman bakyajin magana nana bance kibar gurinnanba dasauri tawuce tabar wurin takoma gefe tatsaya yanufi gindin rariya da abinci yasamu kwano yazuba yasanya ruwa yawanke kaskon sannan yanufi kicin din tana tsaye tana kallonsa yadauki wata tukunya yazuba ruwa yadaura shayi duk tana tsaye tana hangensa yanata kaiwa da komowa acikin gida harya kammala dafa shayin yajuye aflask yanufi kofar gida tana ganin yafice tanufi kicin Don ganin abinda yayi bata hango komaiba tafara bubbude

kwanika cikin tsautsayi bataga flask din yazuba shayinba tabangaje yafado jikake tush flask din yafashe shayin yazube atsakar kicin din tarike baki cike da tsoro dafargaba saita kasa gaba takasayin baya kamar ancilloshi yashigo gidan tundaga nesa ya hangota akicin yakarasa da sauri yana fadin nana meyakawoko kicin dinnan bance kada kisake kishigaba tayi tsuru tsuru daidai lokacin daya karasa yadauki dogon salati sanda yaga flask din shayi duk kwance akasa yana ambaliya ya kalleta yama rasa abinda zaice cikin rawar murya tace Allah yaya bangani bansan da flask agurinba yayi ajiyar zuciya yayi kokarin hadiye fushin shi domin ma'u yargaban goshin shice duk da banzan rawar kanta yanunamat kofa zokiwuce daki maza tataho tana rakube rakube tana goge ido tana gudun kada yadoketa har ta isa bakin kofa data samu tafice ta falla da gudu saida tadire acikin daki sannan tazaya tana haki da dariya wai Allah nagodema da yaya Ahmad ya mini irin ko rankwashinsa ne aida naga takaina tarike haba tana haki shi kam kada kai yayi da takaici sannan ya shiga yashare kicin din yakara dora wani shayin yazuzzuba akofi yakaimata nata hardaki ta amsa tana fadin nagode yaya

23 DAME AKE ADO 2 yadaga kai kawai sannan ya zauna yafara shan nasa ma'u tadubeshi yana shan shayin tace yaya don Allah zankoma makaranta kaga ranar monday za afara jarrabawa kuma Abba yace saikayadda zankoma yadaga kayi yakalleta saiyaga ikacin gaskiyarta take maganar babu wani bayani dazaiyi uagamsada ita saiyace aibazakiyi wannan jarabawarba kihakura kawai tawaro ido cike da fargaba yaya kanufin nadaina karatu kenan kainefa kace zanzama likita yajijjiga kaida damuwa ma'u tayi kankanta da Aure tayi kadan dafuskantar irin wannan matsalolin donhaka gara yasanar da ita gaskiyar komai yadubeta da nutsuwa yace nana kinsan yanzu ke matar aure ce ko? Tadaga kai alamar eh yagyara zama yauwa kinga ai makarantarku ta yanmatace babu matan aure ko? Towannan dalilin yasanya bazaki kara komawaba kinkammala makarantar kenan yanzu zakizauna zaman aurenki kinemi Aljannarki tamike atsorace cike dafaduwar gaba yaya zakace haka yaya Ahmad shikenan niyanzu bazankoma zuwa ko inaba sainan gidan kuma bazan zama likitaba......yaya bakayin karya amman yanzu kayi meyasanya tambayar tacazamasa kwakwalwa harya rasa amsar dazaibata saiyasake hade ransa yace kincikani dasurutu nana tashi maza kiyi wanka kishare gidan kiwanke kwanika tayi narai narai da ido domin tana matukar son karatunta tace amman yaya...............yadaka mata tsawa isaid get out ma'u jikinta yadauki yadauki rawa hawaye yamakale ido yafara tafice dasauri ta

nagoge idonta tana aiki tana kuka yanajiyo sautin kukan nata bashida zabi babu yanda zaiyi abba yagama yanke hukunci daga karshe ma saiyayi wanka yafice yabar gidan wannan shune yakara dagamata hankali saitaji gidan yakara mata girma tazauna tsuru babu abinyi sai tsoro yafara shigarta tamike tanufi soro takama leken waje tana hango mutane dake kaiwa da komowa saitaji sanyi aranta donhaka saita zauna akofar gidan tana kalle kalle dakaramin hijab akanta idan taga abin dariya tayi idan taga abin mamaki tayi mutane suna wucewa suna kallonta babu wanda yayi zaton matar gidance domin komakota basusan ankawo amaryaba sunyi zaton Raliya ce itakuwa daga yanayin kawayenta da gantalin datake fita kullum yasanya suka gano bamatar arzikiceba donhaka babu wani wanda yarabeta tsawon lokaci tananan zaune tana cike da nishadi shikam Ahmad gidansu yanufa kaitsaye yatadda yan uwansa sunzo dayake ranar assabar din karshe sati ce anata cafta saiyazauna anatayi dashi Umma saishige dafice takeyi wurin ganin takammala kirkin rana kunya da nauyi sunhana ta tambayi ma'u takula shima Ahmad kunyar yimata maganar ma'u yake amman daga yanayinsa talura babu wata

matsala anan sukaci abinci lokacin da inna tazuba abincinne ma yatuna da ma'u da abinda zataci saidai Allah yataimakeshi umma tacika flask din da dambu datayi tadire tace gana yar gidanka Ahmadu yaji dadin hakan danyana kammala cin abincin yadauki flask yahaye babur dinsa yanufi gidanshi abinda ybashi mamaki da tsoro baiwuce hangon ma'un shi zaune akofar gida daramba tana hirarta da wasu yara da alama yayan makota tasamu tabiye musu yanacigaba da karatowa mamakinsa nakara linkuwa harzuwa sanda ya iso indatake da babur dinsa tadaga kai takalleshi saitadan firgita masamman yanda yanayinsa yacanza lokaci guda takalli yaran dake gabanta tayi duru duru sai tamike ta shige cikin gida dagudu batayi birki ko inaba saibayan gado tana huci talabe cankurya tana maida numfashi yashigo gidan ransa yana suya ya iso harbayan gadon yajawo kunnenta tafasa ihu jikinta naci gaba da bari dan Allah yaya Ahmad kayi hakuri Uban wa yace kifita waje kizauna komunkoya miji wannan tarbiyar agidane? Cikin sheshshekar kuka tace A ah gidan ne shiru ga tsoro shine naleka waje don Allah kayi hakuri tafashe dakuka yadunkule hannu ya rankwasheta yana fadin koda zanhakura saikinji ajikinki kifita kofar gida kizauna kamar wata sokuwa inakikakai aurenki yakoma rankwashemata kai kwas akanta takuma sanya ihu saida yajeramata guda hudu sannan yasakarmata kunne takuma fashewa dai kuka lokacin yafice daga cikin dakin yanufi shago domin yasanya uniform dinshi yatafi wurin aiki saidai yanashirin kukan ma'u yana dukan zuciyarshi tuncan baya bayason bacin ranta yakanyi komai dankar abatamata rai balle dayaji sunan mahaifiyarsa ne akasanya mata hakan yakara soyayyarta acikin zuciyarsa yanzu kuma gashi tazama matarsa wato yanzu soyayyarta agareshi hawa ukku ce don haka dole intana kuka yarikaji harcikin bargonsa da kyar yakammala shirinsa yanufi soro da zummar yafice saikuma yaga rashin dacewar hakan dan haka yajuya cikin gidan yanufi dakinta tana rakube a inda yabarta abayan gado tana kuka ya isa inda take tahada kai da gwiwa tana sharbe yakira sunana tadago takalleshi dafaduwar gaba don batasan yadawo dakinba tayi zaton kara dukanta zaiyi donhaka tafara ja dabaya tana sharbe majinarta tana kuka

DAME AKE ADO part 11.
24 DAME AKE ADO 2 Dan Allah kayi hakuri wlh bazan kara fitaba nadaina..........yakada kai yana karemata kallo wlh da Abba yayi shawara dashi dazaice abar ma'u takammala karatunta tazama cikakkiyar mace kafin ayimata wannan auren yarinya ce tsaba yanzu tafara kirgen dangi irin namata baikallonta da komai haryanzu sai kanwarsa ihunta yadawoda shi hayyacinsa yace kinga badukanki zanyiba cewa zanyi kidaina fita waje idan nafita zanturo miki yaran sudinga tayaki hira kinjiko? Tadaga kai dagamsuwa tanacew to tuni kukun nata yakoma ciki tafara dariya gawannan idan kinason cin wani Abu kisaya gakuma abinci

can aflask Umma tace akawomiki ta amsa hannu biyu tana godiya yakada kai yafice tabishi dasaikadawo yaya kamar yadda tasaba yimasa agida ya amsa da Allah yasa yafice takalli dari nan tadaka tsalle cike da murna waiyau itace keda dari duk tatace lallai Allah yasanya yara sushigo su siyomata agwalima yayi sa akuwa yan yaran dayatadda azaune dasu har lokacin sunanan zaune suna wasansu don haka yace maza suje sutayata hira dahanzari suka shige gidan suna murna sallamarsu tatsinkayo acikin gidan tayi waje dagudu cike da murna sai alokacin tahango flask din abinci tashiga kicin tadauko faranti tadebi nata suma tazuba masu nasu suka zauna sunaci suna hira itakuma tana kwasar dariya tundaga wannan rana gidan nata yazama gidan yara domin ance laifi yaro kiwa laifin babba rowa Asma'u kam hannunta asake yake akwaita da kyauta Ahmad hankalinsa yakwanta shike hadamusu abinci dazasuci dasafe darana da dare saidai idan yasan yanada aikin safe tun asuba zaidora kirkin rana yazuba aflask ya ajiyemata da daddare kuwa yazomata da ( take away ) domin yace batayi wayon dazatayi girkiba harta kunna risho ba aikinta kawai wanke wanke da shara ko wanki shine kemusu sanda yakeda lokaci saidai yanashan fama da kurciyar ma'u da shirmenta yautunda safe yakammala girkin yazubamata aflask yarufe harya kammala shirinsa tana gindin Tv tana kallon NTA muhawarace akeyi da daliban makarantarsu dana wata makaranta cikin harshen turanci tanajin kamar tatsallake tafada cikin tv idan anyi tambayar dayan makarantar suka kasa amsawa tasani saitayi karaf tace dan Allah kazane kuce kaza ahaka ya isketa tsahon zamani yana kallonta batasan yazoba tausayinta yakamashi ma'u tanason karatu

kwarai shima yanason tayi karatun saidai yanada tsananin kishi bazaitaba yadda ace matarsa tanazuwa makaranta kullumba dama dai ace takammala karatunta akayi aurensu dayaga batada niyyar dawowa hankalinta yakira sunanta tawaiga dasauri tace la yaya harka gama shiri zo dan Allah kaga wadannan sokayen sunkasa amsa tambayoyo nafi sauki kumafa sinio dinmune a school yayi murmushi yace nana nidake sauri zantafi aiki inanakeda lokacin kallo amshi Nan yamikamata kudin tasanya hannu ta amsa yaci gaba da magana zanwuce sainadawo akwai abinci aflask banason barna dawarkai kada kilalata komai kinjiko idankuma andauke wuta kikashe kayan kallo duka dan kada akawo wuta sulalace ta amsa dato tana cigaba da kallonta haryakai bakin kofa baiji tace saikadawo ba yawaiga yakalleta yace yauba babu adawo Ify kanwata dasauri tace lah yaya namanta adawo Ify tana fadin haka tamaida kanta wurin kallonta yayi dariya yafice baijima dafitaba kuma nepa suka dauke wuta bakinciki kamar yakasheta domin taso taga karshen wasan takoma kan kujera takwanta tafara tunane tunanen duniya kwatsam yayarta kuma kishiyarta tafadomata saitaji gaba daya ranta yabaci saidai abinda kedauremata kai baiwuce rashin zuwa gurinta da yaya Ahmad keyiba ko maganarta ma bayayi sam tanason tatambayeshi amman kishi da haushi raliya yahanata don haka tabar abin cikin ranta tana kwance tana sakawa da kwancewa har kawayenta suka fara shigowa tamike tafita suka fara lido A'ilo daya daga cikin yaran ta kalleta tace waike ma'u bakyayin sabon girkine kullum saidai naga kindebo acikin flask ma'u tatabe baki da damuwa ban iya girkinba yayana ne yakeyi yazuba acikin flask A'ilo tace cabdijan to idan bakya gwalgwalawa yaza

ayi ki iya kinganni bankai girmankiba har wake dashinkafa nake dafawa babanmu arisho bama da murhuba mamaki yakama ma'u tace ke A'ilo koni danagirmeki ummana bata bani girkina saitace kazantane saidai kawai na izamata wuta amman kice harwani girki akebaki A'ilo ta tafa hannu tadoki cinya shekarata shabiyu amman wlh ina girki tambayi kanena ma sale idan yashigo saiga sale yashigo da gudu tamkar yasan nemansa ake A'ilo tace yauwa sale zo dan Allah banayiwa ummanmu girki sale yatsaya yana haki kinayi mana ranar har danwake kikayimana ma'u tafe kirji danwake lallai kin iya girki daman inason na iya don allah ya akeyi A'ilo tayi murmushi dadai akwai fulawa ne dasai nanuna miki yanda akeyi ma'u tace bari naduba inada yake ajiye kayan abincin nasa Allah yasanya da fulawar daman nagaji dacin shinkafa da miya ko dafaduka shikenan fa abinda ya iya tanufi dakin taduba ga rashin sa arta bata tadda fulawaba amman saitace ga kudi asiyo gwangwani ukku nafulawa su kwaba dadi ya cika yaran suna murna yauzasuci girkin amarya ihu suke yi tamkar ranar sallah nandai sale yafalle dagudu yasiyo fulawa aka kwada aka kunna risho aka fara kokarin saka danwake gabadaya akaduru akicin din sugoma A'ilo ce agan risho tun ruwan bai tafasaba akafara saka danwake duk sanya daya sai anyi ihu tafi ahaka akammala sakawa aka koma gefe anajiran yatafasa gabadaya danwake ruwa yahadu ya cakude ahaka akafara kokarin saukewa anduba babu tsumman da za asauke ma'u tace bari tasauke bakin zanenta takama tana kokarin saukewa ashe zanin yalaso wuta zafin wutar dayatabota yasanya tafasa ihu tasaki tukunya da zaninta dayakama da wuta nanfa akayi waje ana ihu domin ruwan

danwake yafadi akasa yafallasawa kowa
zanen ma'u yacigaba daci dawuta sukuma
suna ihu gobara! Gobara!gobara haryafara
laso kayan kicin kamar Anjefo shi Ahmad
yashigo agigice jin ihunsu yahango abinda
kefaruwa yakalli ma'u dake ihu daga ita
sai siket duk saiya dimauce yama rasa
mezaiyi candabara tafadomasa yadauki
wani omo da ruwa yanufi kicin dagudu
yafara watsawa dakyar yasamu tamutu
yadawo dabaya yatsaya yana haki saikuma
suka kama ihu wai wutar tamutu takaici
ya isheshi yanufesu afusace yafara dukan
yaran suka sukayi waje aguje afirgice
domin abin yabasu mamaki domin sunsan
duk ihun dasuke baya ce musu kala
amman yau saigashi harda duka yakoma
kan ma'u yazabgamata mari yakoma
zabgamata tafasa ihu tarike kunce
maimakon tabashi tausayi saima kuluwa
yayi yahauta da bala I sai da yayi iyakacin
son ransa sannan yanufi kicin din yafara
gyarawa ranar dai har dare yana bala'i da
masifar dabatasanshi da itaba tayi kum
adaki saikuka washe gari baije ko inaba
yakuma hana kowashigowa gidan duk
yaron dayazo saiya fatattakeshi yafita
dagudu dan haka adaki tawuni tawuni
tanakuka saidai tagama saka abinda zatayi
lokacin daya fita sallar isha'i tadauko
kayanta data kulle adankwali tanufi
hanyar soro tanatafe afirgice cike da tsoro
domin batason kowa yasan inda zata gudu
tagaji dazaman gidan tunda aiba birsina
baceba tafito tajanyo kofar gidan ahankali
tabi gefen duhuwar dake kofar gidan
tafara sauri tana waige don batason wani
yaganta HMMM MUHADU AKASHI NA UKK